
# 'Nine Hanya'



Cikin yan kwanakin nan kai da ni zamu bar wannan duniya – mai yiwuwa ne tafiya ta zo da sauri har fiye da yadda muke zato. Ka san hanyar zuwa sama?

Akwai mutane masu mutunci da yawa wadanda ke zaton zasu iya zuwa sama ta wurin aikata ayyuka masu kyau, ko kuma ta wurin rayuwa mai kyau, ko kuma ta wurin aikin ibada tukuru. Suna sa ran samun shiga sama, gidan Allah, ta wurin aikata ayyuka nagari. Amma wannan ba hanyar Allah ba ce. Duk da irin kyaun wadannan abubuwa da zasu iya aikatawa, ba su bane hanyar zuwa sama wurin Allah.

Yesu Kristi shi ne hanyar zuwa sama, gidan Allah. Yesu ya ce, "Ni ne hanya, ni ne gaskiya, ni ne kuma rai. Ba mai zuwa wurin Uba sai ta wurina" (Yohanna 14:6).

Zunubi guda daya kacal ya sa Allah ya kawar da Adamu da Hawwa'u daga Gonar Aidan har abada. Haka zunubi guda zai rufe maka kofar sama har abada – sai idan ka dogara ga Yesu Kristi a matsayin Mai cetonka. Ka bada gaskiya gare shi? Idan baka bada gaskiya gare shi ba, me za ya hana ka gaskata yanzun nan? Shaidan yana rudinka da cewa, "Ka dan jira kadan." Allah yana fada maka cewa, "Yau ce ranar ceto" (2 Korintiyawa 6:2).

A cikin Littafi Mai Tsarki Allah yana fada mana cewa, akwai wurare biyu kawai da mutane zasu zauna har abada bayan sun bar wannan duniya. Daya daga cikin wuranren nan biyu shine gidan wuta:

"Duk wanda ba a sami sunansa a rubuce a Littafin Rai ba, sai a jefa shi a tafkin nan na wuta" (Ruya ta Yohanna 20:15). "Amma … marasa bada gaskiya … rabonsu yana cikin korama mai ci da wuta da kibiritu; mutuwa ta biyu ke nan" (Ruya ta Yohanna 21:8).

Wadannan ne za su shiga madawwamiyar azaba har abada" (Matta 25:41,46). "Cikin wuta marar kasuwa. A wurin tsutsotsi masu cinsu ba sa mutuwa, wutar kuma ba a kashe ta" (Markus 9:43,44).

Guda wurin da mutane za su zauna har abada bayan sun bar wannan duniya, shine wurin da Ubangiji Yesu Kristi yake da zama, wurin da dukkan wadanda suka karbi Kristi a matsayin Mai cetonsu za su kasance.

"Kada ku damu. Ku gaskata da Allah, ku kuma gaskata da ni. A gun Ubana akwai wurin zama da yawa. Da ba haka ne ba, da na fada muku, domin zan tafi in shirya muku wuri. In kuwa na je na shirya muku wuri, sai in dawo in kai ku wurina, domin inda nake, ku ma ku zama kuna can" (Yohanna 14:1-3). "Kasancewarka takan sa in cika da farin ciki, taimakonka kuwa yana kawo jin dadi har abada" (Zabura 16:11).

Lokacin da Yesu yana nan a duniya ya ce, "Ku

zo gare ni, dukanku masu wahala, masu fama da kayan zunubi, ni kuwa zan hutasshe ku " (Matta 11:28). "Wanda kuwa ya zo gare ni ba zan kore shi ba ko kadan" (Yohanna 6:37).

Yesu, Mai ceto wanda ya tashi daga matattu, a yau yana marmari masu zunubi su zo wurinsa da kukan zunubansu da kuma bukatunsu kamar yadda suka rika zuwa wurinsa lokacin da yake a nan duniya. Idan kai mai zunubi ka zo wurin Yesu Kristi, kuma ka bada gaskiya gare shi a matsayin Mai cetonka, zaka sami alkawarin Allah domin wannan cewa za a gafarta maka zunubanka (duba Ayyukan Manzanni 10:43) kuma zaka je sama gidan Allah kai-tsaye. YESU NE HANYAR ZUWA SAMA, babu wata hanya ko kadan. —*F. W. C. Wurst*

*"Gama Allah ya yi kaunar duniya, har ya bada Dansa makadaici, domin dukkan wanda yake bada gaskiya gare shi, kada ya hallaka, amma ya sami rai na har abada" (Yohanna 3:16).*



Free tracts and biblical counsel available by request. Write:
**Word Of Truth,** P.O. Box 1126, Kaduna, Nigeria.